

# Damuwa lafiya

Hepatites C

## Menene Hepatitis C?

Hepatitis C ciwo ne da kan sami hanta, da hankali har ciwon kan jawo wa hanta kumburi da bac

### Yaya matane ke kamuwa da hepatitisC?

Ana samun ciwon ta wurin jinni da dai duk ruwan da ya fita daga jikin mutum yana kuma kumshe da jinin, in har yana da wanna ciwo kai ma ka kamu da shi. Hanyoyin da jinin ka na iya hadu da na wani sune-

1. Amfani da aluran da wani yayi amfani da shi, ko yin zane da kuma yin amfani da haska ko almakashi ko magogin wani
2. Wasu ababen da ake amfani da su wajen alura kamar su cokali da matatun ruwa
3. Ta hanyar ba da jijin kafin 1990

Ana kuma iya samun kwayoyin ciwon na ta wurin jimai

Kashi biyar zuwa goma ckin dari mata na iya ba jariran su kwayoyin cutar sa'anda suke da juna biyu.

### Menene alamun da kan nuna ko mutum na da hepatitis C?

Mutane da dama masu wannan cutan, ba a ganin alama a jikin su

Canadian AIDS Treatment Information Exchange
Réseau canadien d'info-traitements sida

www.catie.ca

www.apaa.ca

**A yi Shawara na musamman jiyya ta asibiti tare da sanin kwararre likita mai dimbin sanin dangin ciwace ciwace kwayoyin kanjamo da jiyyar su**

Wasu na iya jin rashi lafiya da gajiya a dan lokaci kadan, da mahadin kasusuwan jiki da ciwon ciki ko kuma a ga koren ido ya koma ruwan kwai cikin watani shida bayan kamuwa da ciwon.

Mutane da dama sa warke daga wayanan alamu cikin yan makoni amma wanna bai nuna cewa ciwon ya warke ba.

Bayan shekara kamar goma ko fiye bayan kamuwa da wannan ciwon mutum na iya samun kumburin hanta yana kuma iya samun kansa na hanta

Yaya zan iya sanin cewa na sami wanan ciwo?

Akwai gwajin jinin da akan yi a gane ko kana da wannan ciwo.  Ka nemi shawaran likita game da wannan gwaji.

## Me zanyi in na kamu da hepatitis C?

Hanta mulinmiya gabar jikin mutum ne wanda ke taimakon adana kwayoyin jiki masu kara garkuwar jiki.  Hepatitis C kan bata hanta har ya hana ta akin da ya kamata. Haka ya kamata a tabatar cewa hanta na cikin lafiya kowane lokaci.

Kana iya tabatar cewa hanta na cikin cikaken lafiya ta wurin:

1. Ingatar lafiyar jiki ta wurin cin abincin mai kyau, motsa jiki,hutawa da kuma samun ishashen barci
2. Rabuwa da ababen da na kawo cutar hanta ko kuma rage su – kamar giya, kwayoyin da ke kawo maye, taba da wasu magunguna.
3. Samun aluran rigakafi wanda zai hana kamuwa da hepatitis A da B. Hepatitis C bai da rigakafi.
4. Da taimakon likita ka yi kokarin lura da hantan ka. Wannan na yiuwa ta wurin gwajin jinni.

Akwai magunguna don HepatitisC.  Ya kan zama ta gauraya magunguna iri biyu wato interferon-alpha da ribavirin har tsawon watani goma sha biyu kuma yana warkar da

wasu sarai. Amma akwai wasu matsaloli da wasu kan fuskanta, ka tuntubi likita don Karin bayani.

### Menene kuma zanyi don kula da kaina?

Idan kana da Hepatitis C, kana iya yada shi ga wasu. Don hana wannan

1. Kada ka ba wani jinni ko gabar jikinta ko mani a asibiti
2. Kada ka yi amfani da haska ko magogin baki da wani
3. In kana amfani da magani, kada kayi amfani da alura tare da wani ko ka wanke kayan da jinin ka ya taba, ba zai hana wani kamuwa da shi ba
4. Ka sanar da likitan ka cewa kana da Hepatitis C
5. Ka yi amfani da kororon roba wajen jimai

### Idan ina da kwayoyin Hepatitis C da kanjamau fa?

Hepatitis C da kanjamau in sun hadu, yana iya kawo babban matsala.

Bincike ya nuna cewa masu kwayoyin nan biyu na saurin kamuwa da cututukan da masu kanjamau na kamuwa da su. Saboda haka, duk shawarwarin da muka bayar game da kiyaye kai, ya kamata a lura da su.

Bincike ya nuna cewa masu Hepatitis C da Kanjamau na saurin samun kumburin hanta fiye da masu kanjamua kawai kuma suna iya kasa samun sauki ko sun sha magungunan kanjamau da wasu kan sha su sami sauki

Kamuwa da cututukan nan biyu na iya sa kiwon su yayi wuya domin yawancin magungunan kanjamau na kan kawo wa hanta damuwa. Saboda haka ba kowa ne mai cututukan na biyu zai iya shan magungunan lokaci daya ba. Magungunan da za'a baka sun dangana ga ciwon da ya fi tsanani da kuma yanayin hanta. Ka tuntubi likita game da matakin da zaka dauka.

**Labari mai muhimmanci:**

Masu yada labarai ta jiyyar cuta mai karya garkuwar jiki a kasar Canada da suna CATIE tare da wata kungiya ta Afirka wato APAA, masu aiki akan wanan cuta suna da nufi mai kyau ta wurin hanyar yada labarai zuwa ga masu zama da cuta kwayoyin kanjamo ko cuta mai karya garkuwar jiki, da musamman masu hanyar kula da kansu tare da taimakon ma' aikatan kungiyar da ke jiyya masu wanan cuta.

Labarai da a ka samu ta wurin CATIE ko APAA ba kamar shawaran likita ba ne. CATIE/APAA basu bada goyon baya na musamman jiyya amma masu amfani da mu su yi kokari ta wurin samu shawara da ga wurare masu yawa. Muna kuma karfafa wa masu amfani da mu, su nemi shawara da ga kwararre likita kafin su dauki wani shawara ko amfani da kowane magani.

Ba mu da tabbacin cewa labarai da ga wurin CATIE ko APAA daidai ne.  Harka ce mai hadari idan aka dogara da labarai da ga wurin CATIE ko APPA kawai. Ba za a rike daya a cikin CATIE ko APAA ko ma' aikatan su, shugabannin ko daraktoci, masu taimokon su da laifin diyya akan amfani da labarai da suka yada.

Ra ayin da suke a cikin labarai wanda CATIE ko APAA ta buga na wanda suka wallafa ne, kuma ba ra ayin ko manufa minista mai kula da lafiyan Canada ba ne. Wannan website ya kunshi hadi na waddansu websites. APAA ba ta sarrafa websites da ta hadi ba, APAA ba ta dauki nauyi kayan cikin kowane website da ta hadi tare da website da ta kuma kunshi kowane hadi, ko karuwar da aka yi wa waddanan hadi ta websites. Websites da suka hadi da namu ba su nan a farasanci ko turanci. APAA ta yi tanadi na wannan hadi ta websites domin sauki, ama kunshi ta kowane hadi bai nuna a fakaice APAA ta goyi bayan wannan hadi ta websites ko suna tare da afaretan wadannan websites ba.

Ba mu da tabbacin cewa labarai da ga websites da suka hadi da wannan daidai ne.  Kuma harka ce mai hadari idan aka dogara da labarai da ga nan, a kuma dauki nauyin kallo da yarda da bayani ta farabati da sharrada ta amfani a websites da suka hadi da wannan. Idan za a yi kowane bayani ko bincike akan batun websites da suka hadi da wannan, sai a tuntubi afaretan su

**Copyright**: This Fact Sheet is made available through a collaboration between Africans in Partnership Against AIDS (APAA), Asian Community AIDS Services (ACAS) and the Canadian AIDS Treatment Information Exchange (CATIE). Original content developed by ACAS, 2001. Translation by APAA, 2006.

Funding has been provided by the Public Health Agency of Canada. Supported by an unrestricted educational grant from GlaxoSmithKline in partnership with Shire Biochem.